**EPISODE 11**

**<u>CHARACTERS</u>**

*Tina*

*Hannah*

*Dr. Daoud*

*Laraba*

*Danjuma*

*Nurse Maria*

**EPISODE 11, SCENE 1**

**Northern Kaduna. Danjuma And Hannah's Home. Evening.**

1. **MUSIC:** **<u>THEME MUSIC</u>**
2. **SFX:** **<u>LIGHT MUSIC PLAYING.</u>**
3. **TINA:** Wai Hannah, wannan fim in ya ha*d*u. 'Yan wasan sun burge ni.
4. **HANNAH:** Gaskiya fim in ya ha*d*u, amma ya cika da munafurci da cin amana. Duba yadda aminiyar matar ta ci amanarta. Wannan mumunar abu ne.
5. **TINA:** Haba Hannah, haka rayuwa yake ai. Aminiyar tayi amfani da damar da matar ta bata ne.
6. **HANNAH:** **(LAUGHING)** Hmmm Tina, ina fa jin tsoronki. Tunda kina goyon bayan aminiyar ina ganin cewa ke ma zaki iya yin kowanne abu domin ki cima burinki.
7. **TINA:** Eh mana! Ah Hannah, idanuwa a na bu*d*e suke, ina neman dama.

8. **HANNAH :** Me kike nufi da idanuwanki a bu*d*e suke? Kina nufin kin sa ido akan waccan saurayin ofishinku da kike bani labari?

9. **TINA :** (**LAUGHS)** *K*ilan haka. Hannah ina son in yi miki godiya da kika bani shawara na tsara rayuwata, na "Get it together". Na je asibiti an bani shawarwari.

10. **HANNAH :** Da gaske? Wato kun fara yin nisa da saurayin wajen aikinku kenan Tina?

11. **TINA:** Bari dai na ce wai ina da wata tsari a zuciyata, kuma ba da da*d*ewa ba, zai zama nawa!

12. **HANNAH:** Toh dai ina miki fatan alheri Tina. Amma fa ki yi da hankali, ki yi nazari. Ki tuna cewa "komai nisan jifa *k*asa zai fa*d*o".

13. **TINA:** Toh na gode da shawaranki. **(PAUSES)** Hannah, ina mamaki yadda kike hankali kwance bayan maigidanki na shiga ramin kura kowacce rana.

14. **HANNAH:** (**SURPRISED)** Meyasa kika ce haka kuma Tina? Na ha*d*u da yawancinsu kuma na ga cewa mata masu kirki ne.

15. **TINA:** **(MOCKING)** Hmm zauna nan Hannah, duk sun sa rai akan maigidanki.

16. **HANNAH:** **(SHOCKED)** Meh?!

17. **TINA:** Kalli nan Hannah, sai kin ga yadda suke yi idan sun zo wurinsa … **(PAUSES)** Dakata, kin san sakataren Danjuma?

18. **HANNAH:** Na san ta mana. Tana tare da shi tun lokacin da ya fara aiki a kamfanin. Mata ce mai kirki.

19. **TINA:** Baki da wayo Hannah! Ta fi su duka. Da matsatsan siket nata, da taushin muryarta.

20. **HANNAH:** Tina, ban son wannan maganar. Na san Danjuma, kuma na yarda dashi, na san cewa baya alaka da irin wannan. Yana so na.

21. **TINA:** **(UNCONVINCED)** Toh Hannah, in abun da kika ce ne.

22. **HANNAH:** Tina, me kike so nayi ne? Bazan iya mallakar kan wasu ba.

23. **TINA:** **(IN A LOW VOICE)** Hannah, na san wasu magunguna da man shafawa da zaki iya amfani dasu ki tabbata mijinki ba zai gushe ba. Zan iya kawo miki su.

24. **HANNAH:** **(LAUGHING)** Yanzu na san abun da kike nufi da idonki a bu*d*e suke.

25. **TINA:** Meyasa kike dariya? Ina gaya miki hanyar da zaki ri*k*e maigidanki kuma kina dariya.

26. **HANNAH:** Tina, kar ki damu. Na yarda da Danjuma kuma na san cewa ba zai yi wani abu da zai *b*ata mun rai ba.

27. **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**EPISODE 11, SCENE 2**

**HEALTH CENTRE IN KADUNA NORTH. MIDDAY.**

28. **SFX:** **HOSPITAL AMBIENCE. BRISK FOOTSTEPS. SOUND OFDOOR OPENING AND HITTING AN OBSTRUCTION WITH A THUD**
29. **DR. DAOUD:** **(APOLOGETICALLY)** Wayyo! Nars Laraba! Ina fatan ban ji miki ciwo da *k*ofar ba.
30. **LARABA:** **(STARTLED)** Ah! Ina kwana Dr. Daoud. Yi ha*k*uri, ina son na ajiye maka katin marasa lafiya ne.
31. **DR. DAOUD:** Amma baki ji ciwo ba ko? Na buge ki da *k*ofa, ki yi ha*k*uri.
32. **LARABA:** Kar ka damu Dakta, lafiya nake. Bari na wuce.
33. **SFX:** **SOUND OF FOOTSTEPS GOING OFF MIC**
34. **DR. DAOUD:** Ah Nas Laraba, daman ina son ganinki.
35. **LARABA:** **(SURPRISED)** Ni? Ina fata babu wata matsala Dakta?
36. **DR. DAOUD:** Babu komai. Don Allah ki zauna Nas Laraba.
37. **SFX:** **SOUND OF CHAIR CREAKING AS LARABA SITS**
38. **LARABA:** Ina fatan baka bu*k*atan nayi maka wani abu Dr. Daoud? Domin yanzu na gama ganin marasa lafiyan da ka ce na duba da safen nan.
39. **DR. DAOUD:** Kina da *k*o*k*ari Nas, kuma na amince dake. Ina jin da*d*in aiki tare dake. Kina aikinki ba tare da sai an sa miki ido ba.
40. **LARABA:** **(SHYLY)** Na gode Dr. Daoud.
41. **DR. DAOUD:** **(SOFTLY)** Ina son in baki wannan gorar man gya*d*a. Mahaifiyata ce ta ha*d*a da kanta, musamman domin ke.
42. **SFX:** **SOUND OF CRINKLING OF A NYLON BAG**

43. **LARABA:** **(CONFUSED)** Amma Dr. Daoud, meyasa mahaifiyarka zata yi mun man gya*d*a? Haka take yi wa duk sababbin ma'aikatan kiwon lafiya a inda kake aiki?

44. **DR. DAOUD:** Bata yi. **(LAUGHS NERVOUSLY)** Kin ga, na bata labarinki ne, da kuma yadda nake *d*aukan ki da daraja …

45. **LARABA:** **(EMBARRASSED)** Toh erm… na gode Dr. Daoud. Yayi kyau. Don Allah ka taimake ni kayi wa mahaifiyarka godiya.

46. **DR. DAOUD:** Ya kamata in tabbata cewa sabuwar nas na, mai kuzari, bata da wata damuwa.

47. **LARABA:** Amma bani da wata damuwa. Kuma ni ba sabuwa bace a nan kuma. Amma sai ka kawo mun kyauta kowanne sati Dr. Daoud, ba sai ka yi haka ba.

48. **DR. DAOUD:** Laraba ina jin da*d*in kawo miki wa*d*annan kyaututtuka. Kuma ina son ki ringa kira na Daoud maimakon Dr. Daoud, haka ya dace ko?

49. **LARABA:** "Dr. Daoud" yafi dacewa a wajen aiki.

50. **DR. DAOUD:** Abun da nake fa*d*a kenan. Ina son dangantakarmu ya wuce haka.

51. **LARABA:** **(STUTTERING)** Kana nufin...

52. **DR. DAOUD:** Ina cewa in son mu san juna. Ina son na zo na gabatar da kaina wa mutanenki kamar yadda ya kamata.

53. **LARABA:** **(UNCOMFORTABLE)** Amma Dr. Daoud, na ga cewa yadda muke yayi. Bana son wata soyayya ta shiga tsakani.

54. **DR. DAOUD:** **(HURT)** Meyasa Laraba? Ko baki so na ne?

55. **LARABA:** Ina son ka mana, kuma ina girmamaka. Ina jin da*d*in aiki tare da kai.

56. **DR. DAOUD:** Muna iya *k*arfafa wannan so da girmamawa.

57. **LARABA:** Dr. Daoud, ban tunanin shiga wata soyayya a yanzu. Ina jin da*d*in ‘yan matanci ta.

58. **DR. DAOUD:** Ba fa wasa nake ba, na fa gaya wa iyaye na batunki. Nayi nazari sosai kuma zan ji da*d*i idan kema zaki yi tunani akan wannan maganan.

59. **LARABA:** **(HESISTANT)** Daoud, ban san.....

60. **DR. DAOUD:** Laraba, ba wasa nake ba. Ki yi tunani, kin ji? Sai ki bani amsa anjima.

61. **MUSIC:** **BRIDGE MUSIC**

**EPISODE 11, SCENE 3**

**SOUTHERN KADUNA. HANNAH AND DANJUMA'S RESIDENCE. EVENING**

*62.* **SFX:** **LIGHT MUSIC PLAYING IN THE BACKGROUND**

*63.* **SFX:** **CREAKING SOUND OF BED AS DANJUMA SITS**

*64.* **DANJUMA:** Masoyiyata Hannah, menene labari. Ina fata kina kula da kanki sosai?

*65.* **HANNAH:** Eh kuwa. Ina da gata fa, kalli yadda kake ta ji dani. Na gode da ka wanke kwanukan ko dayake da nayi da kaina.

*66.* **DANJUMA:** **(TEASING)** A'a, tuntuni kike ta aiki. Ina son ki *d*an huta.

*67.* **HANNAH:** **(GIGGLING)** Danjuma, kana *b*ata ni fa. In baka bari ina aiki ba zan yi *k*iba fa. Gashi duk na canza kamanni da wannan juna biyun.

*68.* **DANJUMA:** **(HAPPY)** Kina nan da kyaun ki, kuma In sha Allahu jaririn zai fito lafiyayye, da kyau shima. Ina ta Allah-Allah.

*69.* **HANNAH:** Muna da burin ba wa yaranmu ingantacciyar rayuwa, Allah Ya bamu dama.

*70.* **DANJUMA:** Mu dai zamu yi iya *k*o*k*arinmu. Kuma muna da goyon bayan iyalenmu da abokan arziki wanda ke bamu shawara mu ringa tsara rayuwarmu domin mu cima burinmu.

*71.* **HANNAH:** Kana da gaskiya kuma…

*72.* **SFX:** **PHONE RINGS OFF MIC.**

*73.* **DANJUMA:** Kai! Na manta *d*ayan waya na a falo. Bari na je na *d*auko.

*74.* **SFX:** **DOOR OPENS AND CLOSES.**

*75.* **SFX:** **PHONE MESSAGE TONE BEEPS.**

*76.* **HANNAH:** **(TALKING TO HERSELF)** Wa*d*annan mutanen baza su bar maigida na ya huta ba. Ana kiran wayar dake falo, kuma ga *d*ayan ana aika sa*k*o. Bari na gani.

*77.* **SFX:** **<u>KEYPADS PHONE NOISE.</u>**

*78.* **HANNAH:** **(STILL TALKING TO HERSELF)** Sa*k*o ne daga sakatarensa. **(MUTTERING)** Amma meyasa zata aika masa sa*k*o a cikin wannan daren? Bari na ga me take so.

*79.* **SFX:** **<u>KEYPAD PHONE TONES CONTINUE</u>**

*80.* **HANNHAH:** (**READING ALOUD)** Sa*k*on na cewa: "Na gode sosai Mr D., ina matu*k*ar godiya." **(IRRITATED)** Wace irin sa*k*o ce wannan? Godiyan me take masa? Kuma ita wacece da zata kira maigida na da sunan wasa?! **(PAUSES)** Wai wani Mr D.! Wace irin shirme ne wannan!

*81.* **SFX:** **<u>SOUND OF BED CREAKING AS HANNAH LIES DOWN AGAIN</u>**

*82.* **HANNAH** **(MONOLOGUE)** Ko abun da 'yar uwata Tina ta ce gaskiya ne? Bari Danjuma ya dawo daga amsa waya. Ba zan bar wannan ya kwanta ba.

*83.* **SFX:** **<u>DOOR OPENS AND CLOSES. DANJUMA IS FINISHING A CALL.</u>**

*84.* **DANJUMA:** **(COMING ON MIC, ON THE PHONE)** Toh ranka-yada*d*e. Zamu *k*arasa a ofis gobe. Na gode, sai da safe.

*85.* **HANNAH:** (**SUSPICICIOUSLY)** Sakatarenka ta aika maka sa*k*o a *d*ayan wayanka lokacin da kake amsa waya a falo.

*86.* **DANJUMA:** (**SURPRISED)** Da gaske? Kin duba sa*k*o na ne?

*87.* **HANNAH:** **(SUSPICIOUS)** Kana da abun *b*oyewa ne a wayarka?

*88.* **DANJUMA:** **(SURPRISED)** Babu mana. Wace irin tambaya ce wannan?

*89.* **HANNAH:** (**ANGRILY)** Danjuma , ko kuma na ce Mr. D, menene dangantakarku da sakatarenka da zata yi amfani da sunan wasa tayi maka godiya a cikin wannan daren?

*90.* **DANJUMA:** **(GETTING UPSET)** Sunan wasa?!!! Hannah, menene wannan kuma? Kina hauka ne? Duk *k*ananan ma'aikatan ofishin na kira na da Mr. D.

*91.* **HANNAH:** **(EMBARRASSED)** Oh… **(PAUSES)** Toh dai meyasa sakatarenka zata yi maka godiya da tsakar dare?

*92.* **DANJUMA:** **(UPSET)** Hannah, ban son wannan irin tambayar. Ko dayake na ba wa Mrs Shiga sati *d*aya ta je ta yi jinyar *d*an ta, bayan ta riga ta gama hutun shekaranta. *K*ila abun da take *k*ara godewa ma kenan.

*93.* **HANNAH:** **(DEFLATED)** Oh Danjuma, ka yi ha*k*uri da nayi saurin yanke hukunci.

*94.* **DANJUMA:** Hannah, baki yarda da ni bane? Meyasa zaki yi irin wannan zaton?

*95.* **MUSIC:** **<u>BRIDGE MUSIC</u>**

**SCENE 4.**

**HEALTH CENTRE IN NORTHERN KADUNA. LATE AFTERNOON.**

*96.* **SFX:** **<u>BRISK STEPS ALONG THE CORRIDOR. AMBIENCE OF A CLINIC.</u>**

*97.* _**MARIA:** **(BRUSQUE)** Nas Laraba, don Allah ina iya ganin ki a waje?

*98.* **LARABA:** Toh. Nas Maria, ina fatan ba wani abu ya faru ba?

*99.* **MARIA:** **(CURT)** Ki bi ni waje zaki sani.

*100.* **LARABA:** Toh, muje.

*101.* **SFX:** **<u>BRISK WALK . OUT SIDE NOISE. SOME LIGHT TRAFIC. SOUNDS THE CLINIC (OFF MIC)</u>**

*102.* **LARABA:** Gamu nan a waje. Menene kike son ki gaya mun Nas Maria?

*103.* **MARIA:** Na ganki tare da Dr. Daoud ran nan, kuna zama a ofishinsa kuna ta*d*i. Kaman maganan mai zafi ne.

*104.* **LARABA:** Toh Maria, ban san me kike son na ce ba, amma eh, ni da Dr. Daoud mun tattauna a ziyaransa ta *k*arshe.

*105.* **MARIA:** **(UPSET)** Kalli nan, kar ki nuna mini wani wayo Nas Laraba. Baki san cewa akwai tsari a nan ba?

*106.* **LARABA:** (**GENUINELY SURPRISED)** Wace tsari kike nufi? Na yi wani abu da bai je daidai da tsarin bane?

*107.* **MARIA:** (**BRAZEN)** Eh kin yi Nas Laraba! Baki san cewa ke sabuwa ce a nan, kuma dole ne ki bi *k*a'idodin manyantaka?

*108.* **LARABA:** Ban gane ba. Ki gaya mun abun da kike nufi ki daina kumbiya-kumbiya?

*109.* **MARIA:** (**BITTERLY)** Ina ta shiru ina kallon yadda kike ta matsowa kusa da Dr. Daoud. Kina neman kowanne dama ki zauna tare dashi. Ban san me kike gaya masa ba da yake ta kawo miki kyaututtuka, kuma…

*110.* **LARABA:** **(CUTS IN)** Ki yi ha*k*uri da abun da zan fa*d*a, amma wannan ba ruwanki a ciki. Meyasa kike kallon wa-da-wa yake yi mun kyauta?

*111.* **MARIA:** (**ANGRILY)** Ba ruwana idan wasu maza na baki kyauta, amma da ruwana idan Dr. Daoud ya baki kyauta.

*112.* **LARABA:** Ke ce da Dr Daoud? Bashi da 'yancin kansa ne?

*113.* **MARIA:** **(UPSET)** Kar ki nuna mini wayo! Kowa a asibitin nan ya san Dr. Daoud nawa ne, tun da ya zo nan!

*114.* **LARABA:** Toh Maria, Daoud bai gaya mun wai ke matarsa bace, ko kuma wai kin mallake shi. In kuma hakan take, sai ki gana dashi amma ba da ni ba.

*115.* **MARIA:** *(***SCREECHING)** Nas Laraba baki da kunya! Wa ya ce ki kira shi da sunanshi kwastam, eh?

*116.* **LARABA:** **(CALMLY)** Kalli nan Nas Maria, babu dalilin yin ihu. Ina ganin wannan duk rashin fahimta ne.

*117.* **MARIA:** **(AGGRESSIVELY)** Kalli nan Nas Laraba, ina jan kunnenki. Ki *k*yale Dr. Daoud. Shi nawa ne!

118. **THEME MUSIC AND END CREDITS**